Ba wani wanda aka yi wa rauni a tafarkin Allah face sai ya zo Ranar Alkiyama, raunin nasa yana jini: kalarsa kalar jini, kanshinsa kuma kanshin almiski

Daga Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- zuwa ga Annabi: "Ba wani wanda aka yi wa rauni a tafarkin Allah face sai ya zo Ranar Alkiyama, raunin nasa yana jini: kalarsa kalar jini, kanshinsa kuma kanshinalmiski

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi tsira da amincin Allah yana bayyana mana falalar jihadi a tafarkin Allah Madaukaki da kuma irin abin da mai jihadi ke samu, na lada, cewa duk wanda aka yiwa rauni a tafarkin Allah ko an kashe shi ko ya warke, to zai zo Ranar kiyama gaban al'umma da damarar yaki, zai zo da ciwonsa danye, yana da launin jini kanshin Almiski.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2991